# Shirin Allah domin mutane



## Gabatarwa

Bismillahi.

Cikin Attaura da Zabura da Annabawa, an rubuta shirin Allah zancen Mai Ceton Duniya.

Bayan waɗansu shekaru da yawa, aka rubuta Linjila. A wurin, an rubuta yadda Allah ya aikata nufinsa na cetonmu.

Wani lokaci, su annabawa suka yi zance sai ka ce suna nufin kansu da zamaninsu. To, kai dai, sai ka karanta a hankali, ka duba ko ya yiwu suna zancen wani ne dabam.

# 1

# Budurwa za ta haife shi

Annabi Ishaya ya rubuta cewa: Yanzu fa Ubangiji kansa zai ba ku alama. Wata budurwa wadda take da ciki, za ta haifi ɗa, za a raɗa masa suna Immanuwel. Ishaya 7:14

**Me aka rubuta cikin Linjila?**

Wani manzon Almasihu, sunasa Matiyu, ya rubuta cewa: Ga yadda haifuwar Yesu Almasihu take. Sa'ad da Yusufu ke tashin Maryamu uwar Yesu, tun bai ɗauke ta ba, sai aka ga tana da juna biyu daga Ruhu Mai Tsarki ... Wani mala'ikan Ubangiji ya bayyana a gare shi cikin mafarki, ya ce, Yusufu ɗan Dawuda, kada ka ji tsoron ɗaukar Maryamu matarka, don cikin nan nata daga Ruhu Mai Tsarki ne. Za ta haifi ɗa, za ka kuma sa masa suna Yesu, don shi ne zai ceci mutanensa daga zunubansu. An yi wannan ne duk don a cika abin da Ubangiji ya faɗa ta bakin annabin, cewa, Ga shi, budurwa za ta yi juna biyu, ta haifi ɗa, kuma za a sa masa suna Immanuwel. (Ma'anar Immanuwel kuwa, Allah na tare da mu.) Da Yusufu ya farka daga barci, sai ya bi umarnin mala'ikan Ubangiji, ya ɗauki mata tasa, amma bai san ta ba, sai bayan ta haifi ɗanta, ya kuma sa masa suna Yesu.
Matiyu 1:18, 20–25

Ga inda aka tabbatar da wannan magana kuma: Luka 1:26–56; 2:1–7.

# 2

# Ruhun Ubangiji zai kasance tare da shi

Annabi Ishaya ya rubuta cewa: Ubangiji ya saukar mini da Ruhunsa. Ya zaɓe ni, ya aike ni domin in kawo albishir mai daɗi ga talakawa, in warkar da waɗanda suka karai a zuci, in yi shelar kwance daurarru, da kuma 'yanci ga waɗanɗa ke cikin kurkuku. Ya aike ni in yi shela, cewa lokaci ya yi da Ubangiji zai ceci mutanensa.

Ishaya 61 : 1–2

**Me aka rubuta cikin Linjila?**

Abokin tafiyar wani manzon Yesu mai suna Luka ya rubuta cewa: Yesu ya koma ƙasar Galili, ikon Ruhu na tare da shi. Sai labarinsa ya bazu a dukkan kewayen. Ya yi ta koyarwa a majami'unsu, duk ana girmama shi.

Sai ya zo Nazarat inda aka rene shi. Ya shiga majami'a ran Asabar kamar yadda ya saba. Sai ya miƙe don ya yi karatu. Sai aka miƙa masa Littafin Annabi Ishaya, ya buɗe littafin, ya sami inda aka rubuta cewa,

> Ruhun Ubangiji na tare da ni, don ya shafe ni in yi wa matalauta Bishara. Ya aiko ni in yi shelar saki ga ɗaurarru, da kuma buɗe wa makafi ido, in kuma 'yanta waɗanda ke danne, in yi shela ta zamanin samun karɓuwa ga Ubangiji.

Sai ya rufe littafin ya mayar wa mai hidima, ya zauna. Duk waɗanda ke cikin majami'a suka zuba masa ido.

Sai ya fara ce musu, Yau Nassin nan ya cika a kunnenku. Duk suka yabe shi, suna mamakin maganarsa ta alheri da ya faɗa. Luka 4:14–22

Ga inda aka tabbatar da wannan magana kuma: Matiyu 13:53–54. Markus 6:1–2. Luka 6:17–23; 9:37–43; 13:10–17; 18:35–43; 19:41–44.

# 3

# Abokinsa zai bashe shi

Annabi Dawuda ya rubuta cewa: Har da shaƙiƙin abokina, wanda na fi amincewa da shi, wanda muke ci tare, ya juya yana gāba da ni. Zabura 41:9

**Me aka rubuta cikin Linjila?**

Wani manzon Almasihu, sunansa Yahaya, ya rubuta cewa: Yesu ya san wanda zai bashe shi, shi ya sa ya ce, Ba dukkanku ne tsarkakakku ba.

Na san waɗanda na zaɓa. Wannan kuwa duk don a cika Nassi ne, cewa, Wanda ke cin abincina ya tasam mini. Tun yanzu zan sanar da ku abu tun bai faru ba, don sa'ad da ya faru ku ba da gaskiya ni ne shi. Yahaya 13:11, 18–19

Manzo Matiyu ma ya rubuta cewa: Da magariba ta yi, sai ya zauna cin abinci tare da almajiran nan goma sha biyu. Suna cikin cin abinci, sai ya ce, Hakika, ina gaya muku, ɗayanku zai bashe ni.

Sai suka yi baƙin ciki gaya, suka fara ce dá shi ɗai ɗai da ɗai ɗai, Ni ne, ya Ubangiji? Sai ya amsa ya ce, Wanda muke ci ƙwarya ɗaya, shi ne zai bashe ni. Ɗan Mutum zai tafi ne, yadda

labarinsa ke rubuce, duk da haka kaiton mutumin nan da ke ba da Ɗan Mutum! Da ma ba a haifi mutumin nan ba, da zai fiye masa.

Sai Yahuda da ya bashe shi ya ce, Ko ni ne, ya Shugaba? Yesu ya ce masa, Ga shi kai ma ka faɗa.

Da suka yi waƙar yabon Allah, sai suka fita suka tafi Dutsen Zaitun. Sa'an nan Yesu ya zo da su wani wurin da ake kira Jatsamani. Ya ce da almajiransa, Ku zauna nan, ni kuwa zan je can in yi addu'a. Sai ya komo wurin almajiran, ya ce musu, Har yanzu barci kuke yi, kuna hutawa? To, ga shi lokaci ya yi kusa. An ba da Ɗan Mutum ga masu zunubi. Ku tashi mu tafi. Kun ga, ga mai bashe ni nan ya matso!

Kafin ya rufe baki sai ga Yahuda, ɗaya daga cikin Sha biyun nan, da babban taron mutane riƙe da takuba da kulake, manyan firistoci da shugabanni ne suka turo su. To, mai bashe shin nan ya riga ya ƙulla da su cewa, Wanda zan yi wa sumba, shi ne mutumin. Ku kama shi. Nan da nan sai ya matso wurin Yesu ya ce, Salama alaikum, ya Shugaba! Sai ya yi ta sumbantarsa. Yesu ya ce masa, Abokina, abin da ya kawo ka ke nan? Sai suka matso suka ɗanke Yesu, suka kama shi.

Nan take Yesu ya ce da taron jama'a, Kun fito ne da takuba da kulake ku kama ni kamar ɗan fashi? Kowace rana nakan zauna a Haikalin ina koyarwa, amma ba ku kama ni ba. Amma duk wannan ya auku ne don a cika littattafan annabawa.

Matiyu 26:20–25, 30, 36, 45–50, 55–56

Ga inda aka tabbatar da wannan magana kuma: Markus 14:17–21. Luka 22:14, 21–23. Yahaya 13:21–30. Ayyukan Manzanni 1:15–26.

# 4

# Almajiransa za su yashe shi

Annabi Zakariya ya rubuta cewa: Ka farka, ya kai takobi, ka fāɗa wa makiyayina, ka fāɗa wa mutumin da ke kusa da ni, ka sari makiyayin domin tumakin su watse. Zakariya 13:7

**Me aka rubuta cikin Linjila?**

Manzo Matiyu ya rubuta cewa: Da suka yi waƙar yabon Allah, sai suka fita suka tafi Dutsen Zaitun. Sai Yesu ya ce musu, Duk za ku yi tuntuɓe sabili da ni a wannan dare. Don a rubuce yake, cewa:

Zan buge makiyayi, tumakin garken kuwa su fasu.

Daga nan Matiyu ya ba da labarin yadda aka kama Yesu a Jatsamani, sa'an nan ya ce: Daga nan sai duk almajiran suka yashe shi, suka yi ta kansu.
Matiyu 26:30–31, 56

Ga inda aka tabbatar da wannan magana kuma: Matiyu 26:32–35, 57–58, 69–75. Markus 14:26–31, 50–54, 66–72. Luka 22:33–34, 54–62. Yahaya 18:15-18, 25–27.

# 5

# Za a sa ya sha azaba da kunya

Annabi Ishaya ya rubuta cewa: Na tsiraita ga masu dūkana. Ban hana su sa'ad da suke zagina

ba. Suna tsittsige gemuna, suna tofa yau a fuskata. Ishaya 50:6

Kuma ku karanta Ishaya 52:14; 53:3. Zakariya 13:6.

**Me aka rubuta cikin Linjila?**

Manzo Matiyu ya rubuta cewa: Da gari ya waye sai duk manyan firistoci da shugabannin jama'a suka yi shawara a kan Yesu su kashe shi. Sai suka ɗaure shi, suka tafi da shi, suka ba da shi ga Gwamna Bilatus.

Bilatus ya ce musu, To, ƙaƙa zan yi da Yesu da ake kira Almasihu? Duk sai suka ce, A gicciye shi! Ya ce, Ta wane hali? Wane mugun abu ya yi? Amma su sai ƙara ɗaga murya suke yi, suna cewa, A giccciye shi! Bayan ya yi wa Yesu bulala, sai Bilatus ya ba da shi a gicciye shi.

Sai sojan gwamna suka kai Yesu cikin fadar gwamna, suka tara dukkan kamfanin soja a kansa. Sai suka tuɓe shi, suka yafa masa wata jar alkyabba. Sai suka yi wani kambi na ƙaya, suka sa masa a ka, suka danƙa masa sanda a hannunsa na dama, suka kuma durƙusa a gabansa, suna masa ba'a suna cewa, Ranka ya daɗe, Sarkin Yahudawa! Suka tattofa masa yau, suka karɓe sandan, suka ƙwala masa a ka. Da suka gama yi masa ba'a, sai suka yaye masa alkyabbar, suka sa masa nasa tufafin, suka tafi da shi su gicciye shi. Matiyu 27:1–2, 22–23, 26–31

Ga inda aka tabbatar da wannan magana kuma: Matiyu 26:67–68; 27:11–21, 24–25. Markus 14:65; 15:15–20. Luka 22:63; 23:13–25. Yahaya 18:22; 19:1–3.

# 6

# Aka maishe shi kamar mai laifi

Annabi Ishaya ya rubuta cewa: Da yardarsa ya ba da ransa, ya ɗauki rabon masu laifi. Ya maye gurbin masu zunubi da yawa, ya kuwa sha hukuncin da ya cancanci masu zunubi. Ishaya 53:12

**Me aka rubuta cikin Linjila?**

Luka ya rubuta cewa Yesu ya ce wa almajiransa: Ina dai gaya muku, lalle ne a cika wannan Nassi a kaina, cewa,

An lasafta shi a cikin masu laifi.

Gama abin da aka faɗi a kaina, tabbatarsa ta zo.

Da Luka ya gama shaida yadda aka yi wa Yesu shari'a, ya ce: Wasu mutum biyu kuma masu laifi, sai aka kai su a kashe su tare da shi. Da suka isa wurin da ake kira Koƙwan Ƙai, nan suka gicciye shi, da kuma masu laifin nan, ɗaya a dama, ɗaya a hagun. Luka 22:37; 23:32–33

Ga inda aka tabɓatar da wannan magana kuma: Matiyu 27:38. Markus 15:27–28. Yahaya 19:18.

# 7

# Mutane za su jefa ƙuri'a a kan tufafinsa

Annabi Dawuda ya rubuta cewa: Suka rarraba tufafina a tsakaninsu, suka jefa ƙuri'a a kan babbar rigata. Zabura 22:18

**Me aka rubuta cikin Linjila?**

Manzo Yahaya ya rubuta cewa: Bayan soja sun gicciye Yesu, sai suka ɗebi tufafinsa, suka kasa kashi huɗu, kowane soja ya ɗauki kashi guda. Suka kuma ɗauki taguwa tasa, taguwar kuwa ba ɗinki, saƙa ɗaya ce gudanta. Sai suka ce da juna, Kada mu tsaga ta, sai dai mu yi ƙuri'a a kanta, mu ga wanda zai ci. Wannan kuwa don a cika Nassi ne cewa,

Sun raba tufafina a junansu, taguwata kuwa sai suka yi ƙuri'a a kanta.

Haka fa sojan suka yi. Yahaya 19:23–25

Ga inda aka tabbatar da wannan magana kuma: Matiyu 27:35. Markus 15:24. Luka 23:33–34.

# 8

# Za a yi masa ba'a

Annabi Dawuda ya rubuta cewa: A yanzu dai ni ba mutum ba ne, tsutsa ne kawai, rainanne, abin ba'a ga kowa da kowa! Duk wanda ya gan ni sai ya maishe ni abin dariya, suna zunɗena da harshensu suna kaɗa kai. Suka ce, Ka dogara ga Ubangiji, me ya sa bai cece ka ba? Idan Ubangiji na sonka, donme bai taimake ka ba? Zabura 22:6–8

**Me aka rubuta cikin Linjila?**

Manzo Matiyu ya ce Yesu yana lilo a kan gungumen, sai ga abin da ake yi masa: Masu wucewa suka yi ta yi masa baƙar magana, suna kaɗa kai, suna cewa, Kai da za ka rushe Haikalin, ka kuma gina shi cikin kwana uku, ceci kanka mana! In kai Ɗan Allah ne, to, sauko daga gicciyen mana!

Haka kuma manyan firistoci da malaman Attaura da shugabanni suka riƙa masa ba'a suna cewa, Ya ceci waɗansu, ya kuwa kasa ceton kansa. Ai Sarkin Isra'ila ne, yǎ sauko mana daga gicciyen yanzu, mu kuwa ma gaskata da shi. Ya dogara ga Allah, to, Allah ya cece shi mana yanzu, in dai yana sonsa, don ya ce wai shi Ɗan Allah ne.

Har 'yan fashin nan da aka gicciye su tare ma suka zazzage shi kamar waɗancan. Matiyu 27:39–44

Ga inda aka tabbatar da wannan magana kuma: Matiyu 27:27–31. Markus 15:16–20, 29–32. Luka 22:63–65; 23:11, 35–37, 39. Yahaya 19:2–3.

# 9

# Zai ji ƙishirwa

Annabi Dawuda ya rubuta cewa: Sa'ad da na ji ƙishi, sai suka ba ni ruwan tsami. Zabura 69:21

### Me aka rubuta cikin Linjila?

Manzo Yahaya ya yi zancen Yesu a kan gicciyen cewa: Bayan haka, Yesu da ya san duk an gama kome, don a cika Nassi, sai ya ce, Ina jin ƙishirwa. To, akwai wani gora cike da ruwan tsami a ajiye a nan. Sai suka jiƙa soso da ruwan tsamin, suka soka a sandan izob suka kai bakinsa. Da Yesu ya tsotsi ruwan tsamin nan, sai ya ce, An gama! Sa'an nan ya sunkuyar da kansa ya ba da ransa.
Yahaya 19:28–30

Ga inda aka tabbatar da wannan magana kuma: Matiyu 27:48. Markus 15:36. Luka 23:36.

# 10

# Ba za a karye wani ƙashinsa ba, amma za a huda jikinsa

Annabi Dawuda ya rubuta cewa: Ubangiji yakan kiyaye shi sosai; ba ko ɗaya daga cikin ƙasusuwansa da zai karye ba. Zabura 34:20

Ya kuma rubuta cewa: Kungiyar mugaye na kewaye da ni, suka soke hannuwana da ƙafafuna. Zabura 22:16

Annabi Zakariya ma ya ce: Za su dubi wanda suka soke shi. Za su yi makoki dominsa kamar waɗanda aka yi musu rasuwar ɗan farinsu. Zakariya 12:10

**Me aka rubuta cikin Linjila?**

Manzo Yahaya ya rubuta cewa: Yesu ya sunkuyar da kansa, ya ba da ransa.

Da ya ke ran nan Ranar Shiri ce, kuma don kada a bar jikkuna a kan gicciye ran Asabar (don wannan Asabar ɗin babbar rana ce), sai Yahudawa suka roƙi Bilatus a karya ƙafafunsu, a kuma ɗauke jikkunan.

Sai soja suka zo suka karya ƙafafun na farkon nan, da kuma na ɗayan da aka gicciye tare da shi. Amma da suka zo kan Yesu, suka kuma ga ya riga ya mutu, ba su karya ƙafafunsa ba. Sai dai ɗaya daga cikin sojan nan ya soke shi da mashi a kwiɓi, nan da nan sai ga jini da ruwa suka gudano.

Wanda ya ganin nan kuwa ya ba da shaida kan

haka, shaida tasa kuwa gaskiya ce, ya kuma san gaskiya yake faɗa, don ku ma ku ba da gaskiya.

Wannan kuwa don a cika Nassi ne, cewa, Kashinsa ɗaya ba za a karya ba.

Wani Nassi kuma ya ce,

Za su dubi wanda suka soka. Yahaya 19:30–37

Ga inda aka tabbatar da wannan magana kuma: Yahaya 20:19–29.

# 11

# Za a kashe shi

Annabi Ishaya ya rubuta cewa: Aka ƙware shi ba tausayi, amma ya karɓa da tawali'u, bai ko ce uffan ba. Kamar ɗan rago wanda ake shirin yankawa, kamar tunkiya wadda ake shirin yi wa sausaya, bai ko ce uffan ba. Aka kama shi, aka yanke masa shari'a, aka tafi da shi domin a kashe shi, ba wanda ya kula da ƙaddararsa. Aka kashe shi saboda zunubin mutanenmu. Ishaya 53:7, 8

Kuma ku karanta Zabura 22:14–17

**Me aka rubuta cikin Linjila?**

Luka ya rubuta cewa: Suna tafiya da Yesu ke nan, sai suka cafke wani, mai suna Siman Bakurane, yana zuwa daga ƙauye, suka ɗora masa gicciye, yǎ ɗauka ya bi Yesu.

Wasu mutum biyu kuma masu laifi, sai aka kai su a kashe su tare da shi. Da suka isa wurin da ake kira Kokwan Kai, nan suka gicciye shi, da kuma masu laifin nan, ɗaya a dama, ɗaya a hagun. Sai

Yesu ya ce, Ya Uba, ka yi musu gafara don ba su san abin da suke yi ba. Sai suka rarraba tufafinsa, suna ƙuri'a a kansu.

Sai mutane suka tsaitsaya, suna kallo. Shugabanni kuma suka yi masa ba'a, suka ce, Ya ceci waɗansu, to, ya ceci kansa mana, in shi ne Almasihu na Allah, zaɓaɓɓensa! Soja kuma suka yi masa ba'a, suka matso suka miƙa masa ruwan tsami.

Sai ɗaya daga cikin masu laifin da aka gicciye ya yi masa baƙar magana ya ce, Shin ba kai ne Almasihu ba? To, ceci kanka mana duk da mu! Amma sai ɗayan ya amsa, ya kwaɓe shi, ya ce, Kai ko tsoron Allah ma ba ka yi, kai da ya ke hukuncinka daidai da nasa? Mu kam daidai aka yi mana, don hakika sakamakon aikinmu muka samu, amma mutumin nan bai yi wani laifi ba. Ya kuma ce, Ya Yesu, ka tuna da ni sa'ad da ka zo cikin sarautarka. Yesu ya ce masa, Hakika, ina gaya maka, yau ma za ka kasance tare da ni a cikin Firdausi.

To, wajen tsakar rana ne kuwa, sai duhu ya rufe ƙasa duka, har zuwa ƙarfe uku na yamma. Hasken rana ya dushe. Sai labulen da ke cikin Haikalin ya tsage gida biyu.

Sai Yesu ya ɗaga murya da ƙarfi ya ce, Ya Uba, na sanya ruhuna a hannunka. Da ya faɗi haka kuwa sai ya cika. Sa'ad da kyaftin ɗin ya ga abin da ya gudana, sai ya ɗaukaka Allah, ya ce, Hakika mutumin nan marar laifi ne!

Luka 23:26, 32–36, 39–47.

Wani abokin tafiyar manzanni kuma, sunansa Markus, ya ce: Bilatus ya yi mamakin cewa har ya mutu. Sai ya kira kyaftin ɗin, ya tambaye shi

ko Yesu ya jima da mutuwa. Da ya san haka daga bakin kyaftin ɗin sai ya bai wa Yusufu gawar.
Markus 15:44–45

Ga inda aka tabbatar da wannan magana kuma: Matiyu 27:31–50. Markus 15:20–39. Yahaya 19:16–37.

# 12

# Za a binne shi

Annabi Ishaya ya rubuta cewa: Aka kama shi, aka yanke masa shari'a, aka tafi da shi domin a kashe shi, ba wanda ya kula da ƙaddararsa. Aka kashe shi saboda zunubin mutanenmu. Aka yi jana'izarsa tare da masu laifi, aka binne shi tare da masu arziki. Ishaya 53:8–9

### Me aka rubuta cikin Linjila?

Manzo Yahaya ya rubuta cewa: Yusufu, mutumin Arimatiya, . . . ya roƙi Bilatus izinin ɗauke jikin Yesu. Bilatus kuwa ya ba shi izini, ya kuwa zo ya ɗauke jikin Yesu.

Nikodimu kuma, wanda farkon zuwansa wurin Yesu da dad dare ne, sai ya zo da mur da al'ul a gauraye, wajen awo ɗari. Sai suka ɗauki jikin Yesu suka sa shi a likkafanin linen game da kayan ƙanshin nan, bisa al'adar Yahudawa ta jana'iza.

A wurin da aka gicciye shi kuwa akwai wani lambu, a cikin lambun kuma da wani sabon kabari wanda ba a taɓa kwantar da kowa ba. Da ya ke Ranar Shiri ce ta Yahudawa, kuma kabarin na kusa, sai suka kwantar da Yesu a nan.
Yahaya 19:38–42

Ga inda aka tabbatar da wannan magana kuma: Matiyu 27:57–61. Markus 15:42–47. Luka 23:50–56. Romawa 6:4. 1 Korintiyawa 15:3–4.

# 13

# Za a tashe shi daga cikin matattu

Annabi Dawuda ya rubuta cewa: A kullum ina jin Ubangiji yana tare da ni, yana nan kusa, ba abin da zai girgiza ni. Don haka, cike nake da murna da farin ciki, kullum kuwa ina jin kome lafiya yake, saboda ba za ka yarda in shiga lahira ba, ba za ka bar wanda kake ƙauna a zurfafa daga ƙarƙas ba. Za ka nuna mini hanyar rai, kasancewarka takan sa in cika da farin ciki, taimakonka kuwa yana kawo jin daɗi har abada. Zabura 16:8–11

Kuma ku karanta Ishaya 53:10–12.

**Me aka rubuta cikin Linjila?**

Luka ya rubuta cewa Yesu ya yi annabcin tashinsa daga cikin matattu. Yesu ya ce, Ga shi za mu Urushalima, kuma duk abin da ke rubuce game da Ɗan Mutum ta hannun annabawa zai tabbata. Gama za a bashe shi ga al'ummai, a yi masa ba'a, a wulakanta shi, a kuma tofa masa yau. Za su yi masa bulala, su kashe shi, a rana ta uku kuma ya tashi. Luka 18:31–33

Manzo Matiyu ya rubuta zancen abin da ya faru a kwanakin da suka bi bayan mutuwar Yesu, ya ce: Washegari, wato bayan Ranar Shiri, sai manyan firistoci da Farisiyawa suka taru a gaban Bilatus, suka ce, Ya mai girma, mun tuna yadda mayaudarin nan tun yana da rai ya ce bayan kwana uku zai tashi daga matattu. Saboda haka

sai ka yi umarni a tsare kabarin nan sosai har rana ta uku, kada almajiransa su sace shi, sa'an nan su ce da mutane wai ya tashi daga matattu. Yaudarar ƙarshe za ta fi ta farkon ke nan muni.

Sai Bilatus ya ce musu, Shi ke nan, ku ɗebi soja, ku je ku tsare shi iyakar ƙoƙarinku. Sai suka tafi suka tsare kabarin, suka buga wa dutsen nan hatimi, suka kuma sa sojan tsaro.

To, bayan Asabar, da asussuba a ranar farko ta mako, sai Maryamu Magadaliya da ɗaya Maryamun, suka je ganin kabarin. Sai kuwa aka yi wata babbar rawar ƙasa, domin wani mala'ikan Ubangiji ne ya sauko daga sama, ya zo ya mirgine dutsen, ya zauna a kai. Kamanninsa na haske kamar walƙiya, tufafinsa kuma farare fat kamar snow. Saboda tsoronsa sai masu gadin suka ɗau makyarkyata, har suka yi kamar sun mutu.

Amma sai mala'ikan ya ce da matan, Kada ku ji tsoro, don na san Yesu kuke nema, wanda aka gicciye. Ai ba ya nan. Ya tashi, yadda ya faɗa. Ku zo ku ga wurin da ya kwanta. Ku tafi maza ku gaya wa almajiransa cewa ya tashi daga matattu. Ga shi kuma zai riga ku zuwa ƙasar Galili, a can ne za ku gan shi. Ga shi, na gaya muku.

Sai suka tafi daga kabarin da gaggawa da tsoro, game da matuƙar farin ciki, suka ruga a guje su kai wa almajiransa labari. Sai kuwa ga Yesu ya tarye su, ya ce, Salama alaikum! Sai suka matso suka rungume ƙafafunsa, suka yi masa sujada. Sai Yesu ya ce da su, Kada ku ji tsoro, ku je ku gaya wa 'yanuwana su tafi ƙasar Galili, a can ne za su gan ni.

To, sai almajirai goma sha ɗayan nan suka tafi ƙasar Galili, suka je dutsen da Yesu ya umarce

su. Da suka gan shi sai suka yi masa sujada.
Matiyu 27:62–66; 28:1–10, 16–17

Daga baya, wani manzon Yesu sunansa Bitrus ya ce: Shi Yesun nan fa, an ba da shi bisa ƙaddarar Allah da rigyasaninsa, ku kuwa ƙuka gicciye shi, kuka kashe shi, ta hannun masu zunubi. Amma Allah ya tashe shi bayan ya ɓalle masa ƙangin mutuwa, don ba shi yiwuwa mutuwa ta riƙe shi. Don Dawuda ya yi faɗi game da shi ya ce,

Kullum hankalina na kan Ubangiji, yana hannuna na dama, don kada in jijjigu. Saboda haka zuciyata ta yi fari, ina farin ciki matuƙa. Kuma, ko da yake ni jiki ne, zan zauna ina sa zuciya, domin ba za ka yar da raina a Hades ba, ba kuwa za ka yarda Mai Tsarkinka ya ruɓa ba. Kā sanar da ni hanyoyin rai. Za ka cika ni da farin ciki ta zamana a Zatinka.

Ya 'yanuwa, na iya yi muku magana cikin amincewa game da kakanmu Dawuda, cewa ya mutu, an binne shi, kuma kabarinsa na nan gare mu har ya zuwa yau.

To, da ya ke shi annabi ne, ya kuma san Allah ya rantse masa cewa zai ɗora wani daga cikin zuriya tasa kan kursiyinsa, sai ya hango, ya kuma yi faɗi kan tashin Almasihu daga matattu, cewa dai ba za a yashe shi a Hades ba, jikinsa kuwa ba zai ruɓa ba.

Yesun nan kam, Allah ya tashe shi daga matattu, mu kuwa duk shaidu ne ga haka.

Ayyukan Manzanni 2:23–32

Ga inda aka tabbatar da wannan magana kuma: Luka 24:1–48. Yahaya 20:1–31; 21:1–25. Ayyukan Manzanni 1:1–3; 10:40–41. Romawa 1:3–4. 1 Korintiyawa 15:3–8, 12–20.

# 14

# Zai koma sama

Annabi Dawuda ya rubuta cewa: Ya hau kan tsaunuka tare da ɗumbun waɗanda ya kamo daga yaƙi, yana karɓar kyautai daga wurin mutane.
Zabura 68:18

Kuma ku karanta Ishaya 52:13

**Me aka rubuta cikin Linjila?**

Bayan Luka ya gama zancen tashin Yesu daga kabari, sai ya rubuta cewa: Sai Yesu ya kai su waje har jikin Baitanya. Ya ɗaga hannayensa ya sa musu albarka. Yana cikin sa musu albarka ke nan, sai ya rabu da su, aka ɗauke shi zuwa sama.

Suna cikin dubawa, sai aka ɗauke shi sama, wani gajimare ya tafi da shi, ba su ƙara ganinsa ba. Suna cikin zuba ido sama, shi kuma yana tafiya, sai ga mutum biyu tsaye kusa da su, saye da fararen tufafi. Sai šuka ce, Ya ku mutanen Galili, donme kuke tsaye kuna duban sama? Yesun nan da aka ɗauke daga gare ku aka kai shi sama, zai komo ne ta yadda kuka ga tafiyarsa sama.
Luka 24:50–51, Ayyukan Manzanni 1:9–11

Wani manzon Yesu kuma sunansa Bulus ya rubuta cewa: An ba kowannenmu alheri gwargwadon baiwar Almasihu. Saboda haka Nassi ya ce,

Sa'ad da ya hau sama ya bi da rundunar kamammu, ya kuma yi wa 'yan'adam baye-baye.

(Wato, da aka ce 'Ya hau' ɗin, me aka fahinta, in ba cewa dā ya sauka can ƙasa ba? Shi wanda ya sauka ɗin, shi ne kuma ya hau can birbishin dukkan sammai, don ya cika kome). Afisawa 4:7–10

Ga inda aka tabbatar da wannan magana kuma: 1 Timoti 3:16

# 15

# Zai kasance marar zunubi

Annabi Ishaya ya rubuta cewa: Aka yi jana'izarsa tare da masu laifi, aka binne shi tare da masu arziki ko da ya ke bai taɓa yin laifin kome, ko ƙarya ba. Ishaya 53:9

**Me aka rubuta cikin Linjila?**

Manzo Bitrus ya rubuta cewa: Yesu bai taɓa yin laifi ba faufau, ba a kuwa taɓa jin yaudara a bakinsa ba. Da aka zage shi, bai rama ba, da ya sha wuya kuwa bai yi kashedi ba, sai dai ya dogara ga wannan Mai shari'ar adalci. 1 Bitrus 2:22–23

Kuma Bitrus ya ce wa Yahudawa: Ku kuka ƙi Mai Tsarkin nan, Mai adalci, kuka roƙa a sau muku mai kisan kai, kuka kuwa kashe Tushen Rai, amma Allah ya tashe shi daga matattu, mu kuwa shaidu ne ga haka. Ayyukan Manzanni 3:14–15

Ga inda aka tabbatar da wannan magana kuma: Matiyu 27:1–5. Luka 23:4.

# 16

# Zai sha azaba ya kuma mutu saboda zunubanmu

Annabi Ishaya ya rubuta cewa: Ya daure da wahala wadda a ainihi tamu ce, raɗaɗin da ya kamata da mu ne za mu sha shi. Mu kuwa muna tsammani wahalarsa hukunci ne Allah yake yi masa. Amma aka yi masa rauni saboda zunubanmu, aka daddoke shi saboda muguntar da muka aikata. Hukuncin da ya sha ya 'yantar da mu, dūkan da aka yi ta yi masa, ya sa muka warke. Dukanmu muna kama da tumakin da suka ɓata, kowannenmu ya kama hanyarsa. Sai Ubangiji ya sa hukunci ya auko a kansa, hukuncin da ya wajaba a kanmu.

Aka ƙware shi ba tausayi, amma ya karɓa da tawali'u, bai ko ce uffan ba. Kamar ɗan rago wanda ake shirin yankawa, kamar tunkiya wadda ake shirin yi wa sausaya, bai ko ce uffan ba. Aka kama shi, aka yanke masa shari'a, aka tafi da shi domin a kashe shi, ba wanda ya kula da ƙaddararsa. Aka kashe shi saboda zunubin mutanenmu. Aka yi jana'izarsa tare da masu laifi, aka binne shi tare da masu arziki ko da ya ke bai taɓa yin laifin kome, ko ƙarya ba.

Ubangiji ya ce, Nufina ne ya sha wahala, mutuwar kuwa hadaya ce domin ta kawo gafara; saboda haka zai ga zuriyarsa, zai yi tsawon rai, ta wurinsa nufina zai cika. Bayan shan wahalarsa, zai sāke yin murna, zai fahinta wahalar da ya sha ba ta banza ba ce, shi ne bawana, adali, zai ɗauki hukuncin mutane masu yawa, ya sa su zama

mutanena amintattu. Saboda haka zan ba shi matsayi mai girma, matsayi a cikin manyan mutane masu iko. Da yardarsa ya ba da ransa, ya ɗauki rabon masu laifi. Ya maye gurbin masu zunubi da yawa, ya kuwa sha hukuncin da ya cancanci masu zunubi.
Ishaya 53:4–12

**Me aka rubuta cikin Linjila?**

Luka ya rubuta cewa: Wani mala'ikan Ubangiji ya ce da Filibus, Tashi, ka yi kudu, ka bi hanyar da ta fito daga Urushalima zuwa Gaza, wato, hanyar hamada. Sai ya tashi ya tafi. Sai ga wani mutumin Habasha, wani baba, mai babban matsayi a mulkin Kandakatu, sarauniyar Habasha, shi ne kuwa ma'ajinta, ya zo Urushalima ne yin sujada, yana komawa gida a zaune cikin keken dokinsa, yana karatun littafin Annabi Ishaya. Sai Ruhu ya ce da Filibus, Matsa ka yi kusa da keken dokin nan. Sai Filibus ya yi gudu wurinsa, ya ji shi yana karatun littafin Annabi Ishaya. Ya ce, Kana kuwa fahintar abin da kake karantawa? Sai ya ce, Ina fa? Sai ko wani ya fassara mini. Sai ya roƙi Filibus ya hau su zauna tare. Wannan kuwa shi ne Nassin da yake karantawa:

An ja shi kamar tunkiya zuwa mayanka. Kamar yadda ɗan rago ke shiru a hannun mai saisayensa, haka ko bakinsa bai buɗe ba. An yi masa ƙasƙanci har an hana masa gaskiya tasa. Wa ke iya ba da labarin zamaninsa? Don an katse ransa daga duniya.

Sai baban ya ce da Filibus, Shin kam, annabin nan, maganar wa yake yi? Tasa ko ta wani? Sai Filibus ya buɗe baki ya fara da wannan Nassi, yana yi masa Bisharar Yesu.
Ayyukan Manzanni 8:26–35

Ga abin da Bitrus ya rubuta kuma: Yesu da kansa ya ɗauke zunubanmu a jikinsa a kan gungume, domin mu yi zamanmu matattu ga zunubi, rayayyu ga adalci. Da raunukansa ne aka warkar da ku. Dā kun ɓăce kamar tumaki, amma yanzu kun dawo ga Makiyayi, kuma Mai kula da rayukanku.

1 Bitrus 2:24–25

Manzo Bulus ya rubuta cewa: Jawabi mafi muhimmanci da na sanar da ku, shi ne wanda na karɓo, cewa Almasihu ya mutu domin zunubanmu, kamar yadda Littattafai suka faɗa, kuma cewa an binne shi, kuma cewa an ta da shi a rana ta uku, kamar yadda Littattafai suka faɗa.

1 Korintiyawa 15:3–4

Kuma ku karanta: Romawa 5:6–8. 1 Yahaya 4:9–10.

# 17

# Allah ya cika nufinsa domin mutane ta wurin Yesu Almasihu

Luka ya shaida cewa, bayan tashinsa daga matattu, Yesu ya yi wa waɗansu masu binsa wannan magana: Ya ku mutane marasa fahinta, masu nauyin gaskata duk abin da annabawa suka faɗa! Ashe ba wajibi ne Almasihu ya sha wuyar waɗannan abubuwa ba, ya kuma shiga ɗaukakarsa? Sai ya fara ta kan littattafan Musa da na dukan annabawa, ya yi ta bayyana musu abubuwan da suka shafe shi a dukan Littattafan.

Daga baya Yesu ya sake ce musu: Wannan ita ce maganata da na gaya muku tun muna tare, cewa lalle ne a cika duk abin da ke rubuce game da ni a

cikin Attaura ta Musa, da littattafan annabawa, da kuma Zabura. Sa'an nan ya wayar da hankalinsu su fahinci Littattafai, ya kuma ce musu, Haka yake a rubuce, cewa wajibi ne Almasihu ya sha wuya, kuma a rana ta uku ya tashi daga matattu, a kuma yi wa dukkan al'ummai wa'azi su tuba, a gafarta musu zunubansu saboda sunansa. Za a kuwa fara daga Urushalima. Ku ne shaidun waɗannan abubuwa. Luka 24:25–27, 44–48

Manzo Bitrus ya ce: Ta haka Allah ya cika faɗar da ya riga ya yi ta bakin annabawa duka, cewa dai Almasihunsa zai sha wuya. Saboda haka sai ku tuba, ku juyo, don a shafe zunubanku, Ubangiji kuma kansa ya riƙa wartsakar da ku. Ayyukan Manzanni 3:18–19

Kuma ku karanta Ayyukan Manzanni 4:27–28; 10:34–43; 13:26–41.

**Ko ka roƙi Yesu Almasihu ya zama Mai Cetonka?**

Manzo Bulus ya rubuta cewa: Allah ɗaya ne, matsakanci kuma ɗaya ne tsakanin Allah da mutane —Almasihu Yesu, mutum, wanda ya ba da kansa fansa saboda kowa da kowa. An kuwa yi shaidar wannan a daidai lokacinsa. 1 Timoti 2:5–6

Manzo Bitrus ya yi shaida a kan Yesu Almasihu cewa: Babu kuma samun ceto ga wani. Don ba wani suna duk duniyan nan da aka bayar cikin mutane, wanda lalle ta wurinsa ne za mu sami ceto. Ayyukan Manzanni 4:12

Bitrus ya kuma shaida Yesu cewa: Shi ne duk annabawa suka yi wa shaida, cewa albarkacin sunansa duk mai gaskatawa da shi zai sami gafarar zunubai. Ayyukan Manzanni 10:43

Kuma manzo Bulus ya rubuta cewa: In kai da bakinka ka bayyana yarda cewa Yesu Ubangiji ne, ka kuma gaskata a zuciyarka cewa Allah ya tashe shi daga matattu, za ka sami ceto. Romawa 10:9

Yesu da kansa ya ce: Ku zo gare ni dukkanku masu wahala, masu fama da kaya, ni kuwa zan hutasshe ku. Ku shiga bautata, ku kuma koya a gare ni. Don ni mai tawali'u ne, kuma marar girman kai ne, za ku kuwa sami kwanciyar rai. Don bautata sassauka ce, kayana kuma marar nauyi ne. Matiyu 11:28–30

# Ƙarshen magana

Manzo Bitrus ya rubuta cewa: Annabawan da suka yi annabci kan alherin da zai zama naku, sun tsananta bin diddigi kan wannan cèton, suna bincike ko wanene, ko kuma wane lokaci ne, Ruhun Almasihu da ke zuciyarsu ke ishara, sa'ad da ya yi faɗi kan wuyar da Almasihu zai sha, da kuma ɗaukakar da ke biye.

An dai bayyana musu cewa ba kansu suke bauta wa ba, ku suke bauta wa, game da abubuwan da masu yi muku Bishara ta ikon Ruhu Mai Tsarki wanda aka aiko daga sama suka sanar da ku a yanzu. Su ne kuwa abubuwan da mala'iku ke ɗokin gani. Don haka sai ku yi ɗamara, ku natsu, ku sa zuciyarku sosai kan alherin da zai zo muku a bayyanar Yesu Almasihu. 1 Bitrus 1:10–13

## SANARWA GA MAI KARATU

Ka ga yadda Allah ya cika nufinsa domin mutane sa'ad da ya aiko Yesu Almasihu ya zama Mai Ceton duniya.

Bari ka nemi Littafi Mai Tsarki, ka ci gaba da karatun wannan labari. Wannan dai zai ƙarfafa maka shaida cewa su Attaura da Zabura da Annabawa da Linjila duk suna shaida cewa Yesu Almasihu shi ne zaɓaɓɓe na Allah wanda ya iya cetonka.